# Ka Guji Munanan Sha'awoyi

## Dauda da Bath-sheba—Sashe na 1

**Umurni:** Ka yi wannan aikin a inda babu surutu. Yayin da kake karanta nassin, ka ji kamar kana jin muryoyin mutanen. Ka ji yadda mutanen da ke cikin labarin suka ji. Ka sa labarin ya kasance kamar yanzu yake faruwa.
**Shimfiɗar 'yan wasa:** Dauda, Bath-sheba, Uriah, da Joab
**Taƙaitawa:** Dauda ya yi zunubi mai tsanani kuma ya yi ƙoƙarin ɓoyewa.

### 1 KA YI TUNANIN YANAYIN.—KARANTA 2 SAMA'ILA 11:1-27.

Ka yi zanen da zai nuna nisan kan bene da Dauda ya tsaye zuwa wajen da Bath-sheba take wanka.

Yaya za ka kwatanta halin kowane ɗan wasa a wannan labarin?

Dauda ______

Bath-sheba ______

Uriah ______

Joab ______

Yaya muryar Uriah take yayin da yake magana da Dauda kamar yadda aya ta 11 ta nuna?

______

______

### 2 KA YI BINCIKE SOSAI.

A wace hanya ce kake ganin Joab ya saka hannu a mutuwar Uriah? (*Ka sake karanta aya ta 14-17.*) ______

______

A wace hanya ce Bath-sheba take da laifi a abin da ya faru? (Taimako: *Ka sake karanta 2 Sama'ila 11:4;* sai ka karanta Levitikus 20:10.) ______

______

A ina ne *ya kamata* a ce Dauda yake a lokacin da ya ga Bath-sheba? (*Ka sake karanta 2 Sama'ila 11:1.*) ______

______

Littafi Mai Tsarki ya ce Allah zai ta da mutane da yawa da suka mutu. Waɗanne batutuwa ne za a warware tsakanin Dauda da Uriah da Bath-sheba da kuma Joab?

______

______

______



www.jw.org/ha © 2013 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

Waɗanne dokoki ne Dauda ya karya kuma wane horo ne ya kamata dā an yi masa? (Taimako: Karanta Fitowa 20:13, 14, 17; da Farawa 9:6; Kubawar Shari'a 22:22.) ____________________

A wace hanya ce kuma za a iya ce Dauda ya karya dokar da ke Fitowa 20:15?

____________________

## 3 KA YI AMFANI DA ABIN DA KA KOYA.

Ka rubuta abin da ka koya game da . . .

Haɗarin yin munanan sha'awoyi. (Yaƙub 1:14, 15)

____________________

"Bin umurni" duk da cewa ya saɓa wa dokar Allah.

____________________

Sakamakon zunubi, ko da mai zunubin ko kuma mutane ba su san da zunubin nan da nan ba. (*Ka sake karanta 2 Sama'ila 11:27.*) ____________________

## 4 KA TAMBAYI KANKA.

A wane irin yanayi ne zan iya faɗa wa jarabar kallon abin da zai iya ta da sha'awa marar kyau a zuciyata? ____________________

Ta yaya zan guji yin sha'awar abubuwan da Allah ba ya so? ____________________

Wane darasi ne a wannan labarin ya amfane ni sosai, kuma me ya sa?

____________________

**Shawara:** Ka ba da labarin nan kamar kana nan sa'ad da abin yake faruwa. Ka gana da 'yan wasan da kuma masu kallo.



Ka sauko kuma ka gurza wannan takardar PDF daga www.jw.org/ha



www.jw.org/ha © 2013 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania